# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ’yan Afirka da ke yin ƙaura zuwa Turai
## Kashi na uku: Wasu na kuka, wasu na dariya

Wadda ta rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Lami: | ’yar shekara 20 |
| Malam Talle: | ɗan shekara 60 |
| Matar M. Talle: | ’yar shekara 55 |
| Magaji: | ɗan shekara 22 |
| Faisal: | ɗan shekara 19 |
| Suleman: | ɗan shekara 19 |
| Mai kula da shagon Intanet: | ɗan shekara 30 |
| Sa’adatu: | ’yar shekara 35 |
| Matuƙin jirgi: | ɗan shekara 40 |

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani shirin na "Ji Ka Ƙaru". Wannan shi ne kashi na uku na wannan wasan kwaikwayon namu mai taken "Tudun mun tsira – Mai bayani a kan ƙaurar 'yan Afirka zuwa Turai". A cikin kashi na biyu, kun ji yadda Lami ta fuskanci tsauraran tambayoyi a lokacin da ta tafi neman biza a ofishin jakadanci. Sai dai kuma daga ƙarshe ta yi sa'a ta samu wannan biza. Can kuma a arewacin Afirka, yanzu haka ga Faisal can ya ɓullo da wata dabarar yadda zai tsallaka zuwa Turai ba tare da jami'an tsaro na kan iyaka sun kama shi ba. Sai ku gyara zama domin ku ji yadda za ta kasance a cikin wannan kashin na yau, mai taken: "Wasu na kuka, wasu na dariya". Yanzu dai gari ya waye, kuma rana ta fara fitowa. Ga Faisal can shi da Suleman suna shirye-shiryen wannan tafiya tasu.

**Fitowa ta 1: Faisal da Suleman suna shirin tafiya**

**Faisal:** Haba Suleman, ka hanzarta mana! Mutumin nan da zai yi mana jagora yana waje a mota yana jiranmu. Ka san mun yi latti fa.

**Suleman:** Wallahi kuɗina ne ban gani ba. Don Allah Faisal ka ga *wallet* ɗina? Ka san fa ba zan iya tafiya ba in… in ban ga kuɗina ba ko?

**Faisal:** To, wai don Allah ina ka ajiye ta ne? Don Allah ka yi sauri Suleman! Ka san fa waɗannan mutanen ba sa so su ɓata lokaci.

**Suleman:** Ni dai a nan wajen na san na ajiye ta, amma yanzu ga shi na kasa ganinta. Don Allah Faisal ka gane, ka biya min, in mun isa Turai zan biya ka kuɗinka.

**Faisal:** Wai don Allah wane irin wawa ka ɗauke ni ne? Tun tuni nake jiran wannan ranar, amma na ga alamar so kake ka ɓata min sha'ani!

**Suleman:** Haba Faisal, ni da kai fa abokan juna ne, kuma mun riga mun zama 'yan'uwan juna. Ka taimaka min! A cikin 'yan watanni kaɗan zan biya ka kuɗinka.

**Faisal:** Gaskiya Suleman, ba wani taimako da zan iya yi maka. Ni ma kuɗin da nake da su da ƙyar za su ishe ni. Kuma ka san kuɗin mota ya ƙaru, ko da kuwa ga mutanen da ke kusa da teku. Da ma kuɗin da kowa zai biya shi ne Yuro dubu ɗaya, kuma ni su ke nan gare ni. Sai dai kawai ka yi haƙuri, ni a nan zan bar ka.

**Suleman:** Haba Faisal yaya za ka yi min haka? Ka taimaka! Don Allah ka yi wa direban motar magana, na san zai fahimci halin da nake ciki, zai iya taimaka min!

**Faisal:** Haba Suleman, kar ka wani damu kanka. Kai dai kawai ka yi min addu'a da ni da abokan tafiya. Da zarar mun isa Turai kuma komai ya daidaita, zan aiko maka da kuɗi kai ma ka taho. To abokina, sai wata rana.

**Suleman:** Don Allah Faisal kar ka yi haka! Kar ka tafi ka bar ni!

**Faisal:** Kai! Ku tsaya ni mana. Don Allah ku tsaya!

**Suleman:** Hahahahaha…

**Mai ba da labari:**

Ganin yadda Faisal ya bi motar a guje ya sa Suleman ya fashe da dariya. Sai

dai kuma fa ba wai motar kaɗai Faisal yake bi a guje ba, har ma da mafarkinsa na zuwa Turai. To ko zai cimma wannan motar don ya ci gaba da tafiyar tasa? Sai ku biyo mu.
Can kuma a ɗaya ɓangaren na nahiyar Afirka, ga Magaji yana tsaye a ƙofar gidan su Lami don amsa gayyatar da aka yi masa, kuma don su yi sallama da Lami yayin da take shirin tashi zuwa Turai don ci gaba da karatunta.

**Fitowa ta 2: Magaji ya ci abincin dare a gidan su Lami**

| | |
|---|---|
| **Lami:** | Ina jin wannan Magaji ne ya iso. Don na san ba sa shiri da wannan karen. |
| **Malam Talle:** | Ba wai da kare ne kaɗai ba sa shiri, ni ɗin ma ba shiri muke da shi ba. Allah Ya sa dai ba ta jiyo abin da na faɗa ba. |
| **Lami:** | Ai ni da ma na san da haka, Baba. Bari na je na buɗe masa ƙofa. |
| **Malam Talle:** | E, je ki buɗe masa! |
| **Lami:** | Kai Sporty, bari mana! Magaji ne ba ka gane ba? |
| **Magaji:** | Don Allah tambaya nake, wai nan ne gidan su Lami? |
| **Lami:** | Gaskiya ba nan ba ne, ɗan samari. Ina ganin ɓatan-kai ka yi. |
| **Magaji:** | Gaskiyarki, 'yammata. Ba dole na yi ɓatan-kai ba tun da ba na tare da ita? |
| **Lami:** | Ina gani ita ma dole ta yi ɓatan-kai idan ba ka tare da ita. |

Yi maza ka shigo, ga su Baba can suna jiranka.

**Magaji:** Baba, an wuni lafiya?

**Malam Talle:** Lafiya lau. Yaya dai Magaji? Shigo daga ciki mana. ... Ranki ya daɗe, duk mun haɗu, ke kaɗai ake jira.

**Matar M. Talle:** Magaj,i sannu da zuwa. Abin da za a yi shi ne kowa zai zuba wa kansa. Don haka kowa ya ɗiba son ransa.

**Magaji:** Mmm… duk ƙanshi ya game wurin kuwa!

**Malam Talle:** Magaji, wai yanzu me kake ciki ne?

**Magaji:** Gaskiya ni yanzu ba ni da wani shiri da nake yi tun da kwanan nan na gama jami'a.

**Matar M. Talle:** Shin ba ka son kai ma ka ci gaba da karatun ne?

**Lami:** Don Allah mu koma wani zancen mana.

**Magaji:** E tabbas, Mama, zan so haka. Sai dai kuma gaskiya a yanzu ba ni da hali saboda iyayena ba za su iya biya min ba. Kuma har yanzu ƙannena ba su gama makaranta ba. Dole ne na samu aiki don na taimaka wa iyayena da 'yan'uwana.

**Lami:** Da Magaji fa za a tafi idan za a raka ni zuwa *airport*.

**Matar M. Talle:** Oh, da shi za a tafi ke nan?

**Magaji:** Da ni kuma?

**Malam Talle:** Tabbas, me zai hana. Ai kai ma ka zama ɗan gida.

**Magaji:** Na gode! Wallahi kun kyauta.

**Lami:** Kun san fa da zarar na dawo daga karatuna, za a ɗaura mana aure.

**Mai ba da labari:**
Wannan magana da Magaji ya ji daga bakin Lami ta ba shi mamaki, balle ma kuma iyayenta. Amma kuma sai wannan mamaki ya rikiɗe ya zamo farin ciki. Bayan 'yan kwanaki na jiran tsammani sai ranar tashin Lami ta zo. Yanzu dai ga ta nan da iyaye, da 'yan'uwa, da abokan arziƙi, da kuma abokan karatunta, duk sun rako ta, cikinsu kuwa har da Magaji. Amma kafin mu ga tashinta zuwa Turai bari mu ji yadda a can kuma Faisal yake juyayin rashin samun tafiyarsa zuwa Turai. Tun dai daga wannan rana bai sake haɗuwa da abokinsa Suleman ba. Sai dai kuma ga alamu suna dab da cin karo da juna a wani shagon intanet.

### Fitowa ta 3: Faisal ya gamu da Suleman a shagon Intanet

**Faisal:** Barka da aiki!

**Mai kula da shagon Intanet:** Yauwa, barka kadai, Malam.

**Faisal:** Ina son yankar tikiti.

**Mai kula da shagon:** Na awa nawa?

**Faisal:** Na rabin awa.

**Mai kula da shagon:** To, ga su. Je ka hau kan kwamfuta lamba uku daga can

gefen hagu. Amma kafin nan kawo kuɗinka tukuna.

**Faisal:** To shi ke nan, ga shi.

**Suleman:** La! Faisal, wa nake gani? … Don Allah ka yi haƙuri da abin da…

**Faisal:** Ka ga Suleman, yanzu ba lokacin wannan maganar ba ne. Ma yi magana daga baya idan na gama abin da nake.

**Suleman:** In ce dai ba fushi kake da ni ba ko?

**Faisal:** Haba, yaya zan yi fushi da kai? Ai komai yana da dalili. Wataƙila ba a wannan lokacin Allah Ya ƙaddara tafiyata ba.

**Suleman:** Ka ga fa maganarka na iya zama gaskiya. Ba mamaki jinkirin ya zame mana alheri.

**Faisal:** Na ji, na ji, Allah Ya sa hakan! Amma don Allah ka ɗan jira ni a nan, yanzu zan dawo.

**Mai ba da labari:**
Waɗansu mutane dai a duniya Allah yakan nufe su da samun iyaye masu arziƙi ko masu rufin asiri, wato dai kamar irin su Lami. Waɗansu kuma kamar su Magaji ba su samu wannan damar ba. Waɗansu kuma kamar su Faisal da Suleman, abin dai sai a hankali, don kuwa rayuwar ta yi tsauri da yawa. Don haka zaɓin da suke da shi kawai shi ne su nufi inda rayuwa take da ɗan dama-dama. Wannan ta sa Faisal bai yi wata-wata ba wajen sake shirya wata tafiyar. A wannan karon ya haɗu ne da masu safarar mutane, wato masu sumogal ɗin mutane zuwa Turai ba bisa ƙa'ida ba, matsawar dai za a biya su. Daga ɗaya ɓangaren kuma ga Lami can tana zaune a cikin jirgi cikin fargaba. A kusa da ita kuma ga wata mata nan mai suna Sa'adatu 'yar shekaru kamar

talatin, wadda ke auren wani Bature, wadda kuma za ta koma Turai bayan ta ziyarci danginta.

**Fitowa ta 4: Lami da Sa'adatu a cikin jirgi**

**Sa'adatu:** 'Yammata, ga alamu dai wannan shi ne hawa jirginki na farko, ko?

**Lami:** Gaskiya ne, wannan shi ne na farko.

**Sa'adatu:** To idan dai haka ne, kar ki ji komai, za ki ji daɗinsa. Yauwa! Ni sunana Sa'adatu, amma kuma akan kira ni da Sa'a.

**Lami:** Ni kuma sunana Lami Talle.

**Sa'adatu:** Na yi farin cikin haɗuwa da ke wallahi. Hala dai… saurayinki za ki ziyarta ko?

**Lami:** A'a, na riga na yi sallama da saurayina a *airport*. Ni yanzu Turai na nufa don ci gaba da karatuna.

**Sa'adatu:** Lallai! Abin ya yi! Da ma abin da nake nufi ke nan, ba wai zancen saurayi ba. Amma na san dukkanku kun ji ba daɗi ko?

**Lami:** Gaskiya kam ba daɗi. Amma mun shirya idan na dawo daga karatuna za a ɗaura mana aure.

**Sa'adatu:** Lallai! To, yaushe kuma za ki kammala karatun naki?

**Lami:** Nan da shekara uku. Zan yi karatun lauya ne.

**Sa'adatu:** Shekara uku! Lallai!

**Lami:** Kina ji ko Sa'adatu, na san dai haɗuwarmu ke nan, amma wallahi rigar nan taki ta burge ni. Ga takalman nan naki da kuma abin wuya, abin dai ba magana.

**Sa'adatu:** Allah ko Lami? Na gode. Ai kuwa ba ki sani ba, ni ma wallahi daga ganinki sai na ji ina ƙaunarki. Kuma saboda haka ne ma zan ba ki lambar wayata ko da za ki buƙaci wani abu, ko kuma idan kina son fita shan iska da abokanki, sai ki kira ni. Kin ji?

**Matuƙin jirgi:** Jama'a, muna yi muku maraba da hawa wannan jirgi namu mai lamba 7896. Sunana Kyaftin Kande. Yanzu dai haka wannan jirgi yana shirin tashi, don haka sai kowa ya ɗaura bel ɗinsa sannan kuma ya tayar da kujerarsa tsaye. Kuma masu taimaka wa fasinjoji sai ku koma kan kujerunku don kuwa za mu tashi.

**Lami:** Madalla, na gode.

**Sa'adatu:** Ba komai wallahi. Allah Ya sauke mu lafiya.

**Lami:** Amin.

**Mai gabatarwa:**
To masu sauraro, a daidai lokacin da Lami ta tashi sararin samaniyar Afirka zuwa Turai ne, muka kawo ƙarshen kashi na uku na shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan yadda matasan Afirka ke ƙaura daga nahiyar zuwa Turai. Ga alamu dai Sa'adatu ta samu karɓuwa a gurin Lami, anya wannan matar abar amincewa ce kuwa? A can kuma Afirka ta Arewa ba mu san wane shiri Faisal ya sake yi

ba, bayan da ya kasa samun nasarar tsallakawa zuwa Turai tare da sauran abokansa 'yan gudun hijira.
Duka dai za ku ji yadda za ta kaya a cikin kashi na gaba na shirin namu. Kuma kuna iya tuntuɓarmu a dandalin tattaunarwamu da ke adireshinmu na facebook.com/dw.Ibe don tattauna yadda irin jimamin da mukan ji idan muka zo yin ban-kwana da wani daga cikin 'yan'uwa da abokan arziƙi ko kuma waɗanda muke ƙauna a yayin da suke shirin yin ƙaura zuwa wani muhallin. Kafin nan, sai mu ce, Allah Ya ba mu alheri.